






Mu duba inda muke.

Akwai abubuwa a

kewaye da mu.

Wasu na da rai.

Wasu basu da rai.

Buta ba ta da rai.

Benci ba shi da rai.

Tebur ba shi da rai.


Riga ba ta da rai.

Wando ba shi da rai.

Hula ba ta da rai.








Aji ba shi da rai.

Allo ba shi da rai.

Alli ba shi da rai.




Kofa ba ta da rai.


Kofi ba shi da rai.

Kwali ba shi da rai.











Dutse ma ba shi da rai.

Wuƙa ma ba ta da rai.

Randa ma ba ta da rai.

Abu mara rai ba ya ci.
Abu mara rai ba ya sha.
Abu mara rai ba ya ji.



Abu mara rai ba ya motsi.

Abu mara rai ba ya girma.

Abu mara rai ba ya gani.